# Cigaban Kasa

TATTALIN ARZIKI

**Bukata: Kyakkyawar Manufa, Ba Agaji Ba** **1min 53 secs** **5**

*Kasashe masu tasowa dake bukatar agaji, zasu fuskanci mawuyacin hali wajen samun agaji daga kasashen dake bada taimako na duniya.*

**Shin Gwamnati Tana Kashe Abunda Ya Kamata?** **2mins 8 secs** **3**

*Abinda Gwamnati take kashewa domin cigaban kasa, kwalliya bata biyan kudin sabulu kan tattalin arkikin kasa.*

**Kasashen Gabashi Sun Sami Agaji Fiye Da Na Kundanci A Shekarun 1990s** **2 mins 26 secs** **4**

*An kawo karshen mahawararda ta mamaye wadan nan shekaru*

MATA

**Shekaru Biyar Bayan Taron Beijin** **1min 38 secs** **14**

*Mata sun matsawa gwamnati lamba a karon karshe domin kawo karshen nuna bambancin da akeyi tsakanin maza da mata.*

**Birnin Da Akafi Yiwa Mata Fyade A Duniya** **1min 31 secs** **15**

*Afrika ta kudu ta cira tutar cin zarafin mata a duniya.*

**Tozartar Da Mata a Sassa Daban-Daban Na Duniya** **1min 26secs** **14**

**Munanan rahotanin cin zarafin mata a wasu kasashen duniya**

KWADAGO

**Ma'Aikata A Kasar Mali Sunyi Nasarar Samun Karin Albashi** **3 min 30 secs** **8**

*Ma'aikatan Mali sunyi nasara kan yajkin aikin da sukayi*

**Kungiyoyi** **2min 17secs** **13**

*Kugoyoyi masu zaman kansu, suna kalubalantar kokarin da Gwamnati keyi na matse su.*

# Yanahin Muhalli

**Tsarin Kula Da Kare Muhalli** **15secs** **13**

*Rashin Sani da bambanci na barazana ga tsarin muhalli*

**Madagasca Ta Kaddamar Da Sabon Gandun Daji Na Kasa** **3 mins 11secs** **10**

*Yanki kudu maso gabashin Madagasca yakai ga wurin yawon bude ido*

**Muhimman Hotunan Hallitu A Na'urar Zamani** **1min 30 secs** **3**

*Yanzu za ka iya ganin muhimman hotunan hallitu iri-iri ta hanyar amfani da na'urar Internet.*

**Saran Itatuwa Ba Bisa Doka Ba Na Barazana Ga Dazuzukan Tanzania** **2mins 19 secs** **6**

*Gandun da jin kasar Tanzania da yakai kadada miliyan 33 na fuskantar karuwar barazana.*

**Gurbacewar Yanayi** **2mins 13 secs** **5**
*Kasar filifins na dubar sabo sabuwar dabarar kula da shara manila ta dukufa wajen samo sabuwar dabarar sarrafa shara, ganin tschuwar dabarar da take bi ta citura*

NAMUN DAWA
**Ghana Na Fama Da Raguwar Kifi Cikin Hanzari** **4 mins** **7**
*Karuwar dabarun kamun kifi irin na zamani ya sanya yawan kifin da Ghana ke dasu na raguwa wasu irin ciyayi masu dafi na barazana ga filaye a gabashin Afrika Ciyayin da aka sansu a sashin gabashin Afrika yanzu sun fara mutuwa saboda wata irin ciyawa mai dafi.*

## Sashin Yara

**Lokutan Da Bauna Ke Farauta** **5mins 10 secs** **11**
*Hadama ta sanya Bauna ta rasa rawanin sarautar sarkin Dawa ga Zaki.*
**Rezar Mikiya** **2mins 7 secs** **13**
*Mikiya da Hankaka da kawaye ne amma saboda batan reza, sai suka bata.*
**Meyasa Kuma Yaya Ne Jalbe Ke Yin Kofa A Busashen Itace** **1 min 2 secs** **12**
*Sadu da tsun tsun dake huda busashen itace domin yin gida.*
**Ta yaya Karkanda ke kare kan sa DagaAbokan Gara?** **1 min 11sec** **12**

# Labaru

**Gwamnati Tana Kashe Abu Mai Kyau? 2min. 8secs**

Zai baiwa akasarin 'yan Afrika mamaki da jin cewar kudaden da Gwamnati ke kashewa na tauye cigaban tattalin arziki. Binciken da wata kungiya dake Biritaniya mai suna kungiyar nazarin cigaba DSA ta gudanar ya nuna cewa kashe kukaden Gwamnati kan aiyukan da ba na samar da kayayyaki ba ko na cin jama'a ba na dakile tattalin arziki. Wannan kuwa yafi baiyana a kasa irin Najeriya, inda harkoki duk sunfi ta'allkewa kan kwangila daga gwamnati. Kwangila na karfafa gwiwar shigo da kaya waje, kamar kayan aiki da kwaraun da zasu aiwatar da aikin. Domin haka tattalin arziki baida wani tasiri akai.

Binciken kan tattalin arziki an gudanar dashi ne a kasar Tanzaniya kasar da ta zama zakaran kwaji, wadda take fafutuka duk da irin bukatun jama'ar ta dakuma dan arzikin ta kalilian. Daga cikin irin abinda binciken ya gano sun hada da, kashe kudade a kasashe masu tasowa na tattare da gibin kasafin kudi, dakuma nawa kan cigaba. Haka kum,a nazarin ya gano cewa rage kashe kudin gwamnati zai taimaka wajen bunkasuwar tattalin arziki.

Nazarin ya gano cewar akwai wasu manyan hanyoyin kashe kudi a kasashe masu tasowa, kamar, kashe kudi wajen zuba jari, aiyukan da basa tsinana komai dakuma kashe kudi kan harkokin jama'a..

Daga ciki an gano kashe kudi kan zuba jari shine ke da rashin amfani ga tattalin arzikin kasashe masu tasowa. Wannan kuwa da mamaki, domin anan ake saran samun karuwar tattalin arziki, amma maimakon haka shi yafi dakile tattalin arzikin. Amma kashe kudi kan harkokin jama'a irin si. Kiwon lafiya da ilmi sukan kai ga karuwar tattalin arzikin.

Domin habaka tattalin arziki, Gwamnatocin kasashe masu tasowa kamata yayi su maida hankali wajen bada ilmi da inganta kiwon lafiya. Haka kuma tilas su karafa gwiwar'yan kasuwa domin zuba jari kan harkokin kasuwanci. Wannan sabuwar canjin maufar kamati yayi a bita da yekuwar samar da yanayi mai kyau wanda zai janyo hankalin masu zuba jari daga waje.
*ID21/Obasi Ogbonnaya*

**Muhimman Hotunan Halittu A Bukin Baje Koli 1min 30 secs**

Sama da hotuna dubu goma ne na halittu iri-iri wata kila shine mafi girma da ban mamaki a duniya nan gaba kowa zai gan su a ko ina kake a duniya da zarar ka matsa butur. Wannan kuwa hukumar kare hallitu ta duniya WWF da kamfanin na'urar kasuwanci ta duniya CANON ne zsau samar.

Wajen bukin baje kolin litattafai na musamman a Frankfurt ranar 15 ga Oktoba kungiyoyin biyu zasu kaddamar da abinda suka kira bisa tsarin hotunan muhalli. Hotunan zasu kai ga jama'a ta hanyar na'urar Internet kafin tsakiyar shekarar 2000.

Amma kugiyar kula da muhalli tana iya yin amfani da hanyoyin ta na cikin gida domin kiran Internet wajen samun hotunan domin fara aiyukan ta, na ilmantarwa da kuma na yekuwa.

Hotunan sun kunshi dubban hotunan da akayi ta dauka ne tun shekarar 1964, wadanda wasu masu daukar hoto su dari biyar sukayi a sassa daban daban na duniya. Sanarwar da aka bayar game da hotunan tace wannan somin tabi ne daga abinda zai biyo baya. Hotunan sun kunshi yekuwar muhalli da aiyuka da hatsarin da wasu halittu ke fuskana da irin matakan da yanzu haka ake dauka.

Wannan zai kara bisa sabuwar hanyar da aiyukan WWF ke samarwa ga kwararu kan aikin watsa labarai a duniya inji sanarwar.
*WWF*

**Kasashen Gabas Sun Sami Agaji Fiye Da Na Kudanci**
**A Shekaun 1990s 2min. 26secs.**
Fargabar da kasashen Afrika da sauran masu tasowa keyi na cewar agaji zai koma gabashin Turai bayan faduwar taryyar Soviet ya tabbata. Tabbacin kuwa yazo ne kusan shekaru goma bayan da kasashen Afrika suka koka, amma kasashen turai suka ki yarda.

Tabbacin yazo ne cikin kasidar da aka gabatar. Kasidar tayi kan babban dalilin canja alkibla wajen bada agaji da Kasashen Turaix dake bada agaji tattalin arziki (OECD) sukayi a shekarun 1990s. Ta baiyana cewar akwai raguwar bayar da agaji daga kungiyar (ODA) daga kudanci zuwa gabashin Turai saboda a wannan lokacin kungiyar bayar da agaji ta OECD ta karkata hankalin ta.

Akasarin kasashe masu tasowa ana dangantasu ne da kasashen dake kudanci domin suna kudu ne da layin da ya raba duniya gida biyu.

Rahotanin hukumomi daga kungiyar ta OECD sun nuna cewa babu canjin alkibla da aka samu tsakanin 1990-94 zuwa gabashin Turai, amma agaji zuwa yankin na gabas na kara samun sa ido. Saidai kuma wasu rahotanin suncecanje-canje sun inganta yadda ake bayar da agajin daga afrika zuwa gabashin Turai dakuma yawan raguwar bayar da agajin da ake baiwa kasashen Afrika.

Haka kuma kungiyar nazarin cigaban kasar ta gano cewa anyi canji a hukumar OECD kan ma’anar agaji ta yadda zai kunshi taimakon warware matsalolin dake cima duniya tuwo a kwarya. Wannan kuwa ya sabawa hanyar da aka saba bi wajen bayar da agaji domin cigaban kasa. Wannan canji bisa sabuwar gabar da ta bulla bayan yakin cacar baki tsakanin kasashen dake bayar da agaji sun isa dalilan da ya sa suka rage bayar da agaji ga kasashen dake kudancin duniya.

Kungiyar ta bada shewarwari kan matakan da za abi domin shawo kan matsalorin.

- ? A raba kudaden taimakon warware matsalolin dake addabar da kudin da aka bayarwa domin aiyukan raya kasa.
- ? Haka kuma kungiyar OECD na iya canja ma’anar agajin raya kasa ta yada zai hada da kudin da ake bayarwa domin warware matsalolin dake addabar duniya.
- ? Da kuma kyale jami’an bincken kudade masu zaman kansu surika binciken kudaden da aka samu daga kasashe masu bada maimakon kasashen da suka bada agajin surikayi da kansu .

*DSA*

**Kasar Filifin Na Dubar Sabuwar Hanyar Sarrafa Shara 2 mins 13 sec**

Birnin manila hedkwatar kasar filifins dake kudu maso gabashin Asia ta kafa doka abota wajen sarrafa shara ga mazauna. Birnin. Dokar ta bukaci dukkan masu daukar shara da su raba jakunan sharar zuwa launi hudu. Bakar jaka domin daukar dottin da bai shafi magunguna ba, Tsanwar jaka dottin makanikai jar jaka dattin masana'antu mai guba jaka mai launin rawaya domin dottin da bai danganci magunguna cutuka masu yaduwa,. Wadanda za arika tarawa a wurin tara sharar brinin.

Wannan sabuwardokar tazo ne a daidai lokacin da wuraren tara sharar manila ke cika kuma ana kokarin rufe suba akuma samu wasu sabbin wuraren tara sharar ba wani jami'in huumar raya birnin manila ya bukaci dokar da ta rika sa ido wajenzubar da sharar domin kaucewa matsalar dake tattare da hakan.

Masu hangen abinda kaje yazo sun soki wannan sabuwar dokar wanda suka ce bata da tasiri. Sunce dokar bata fayyace hanyoyin da za a sarrafa sharar ba. Manila dai na kona sharar da ake tarwa ne yayinda kuma ake binne wasu a kasa. Amma hukumomin birnin sun kuduri aniyar daina amfani da hanyar kona shara yazuwa shekara ta 2003, wanda zai bukaci samar da ma'aikatun sarrafa sharar.

Sauran matsalolin da dokar ke fuskanta sun hada da kudin da masu gidajen zasu rika sayen jakuna masu launi kimanin dalar Amurka daya kan jakuna 20, da kafa wurin ajiye shara dakuma hukuncin da za arika yiwa duk wanda ya fidda jakunan sharar kafin isowar motar daukar sharar ta iso. Tarar tana kamawa ne daga dalar Amurka 25 ko daurin wata shida. Duk da wadan nana matsalolin akasarin masu gidaje sunce tuntuni yakamata wannan dokar ta fara aiki. Suna fatan hakan zai karfafa gwiwar tarawa da sake sarrafa sharar dakuma binnewa a karkashin kas. Kamata yayi wasu biranen Afrika suyi nazari da wannan sabuwar dokar ta manila domin wasu daga cikin sassan dokar zasuyi amfani ga kasashen Afrika.

**Abin Bukata: Kyakkyawar Manufar Tattalin Arziki Ba Agaji Ba 1min 53 secs**

Kasashe masu tasowa Zasu fuskanci wahaloli wajen samun taimakon kasashen duniya domin habaka aiyukan su na raya kasa a nan gaba. Tilas su tsammaci taimako kalilan na kudi tare da koyon darasi mai yawa kan manufofin da za subi wajen kara inganta tattalin arziki su daga kasashen dake bada taimako.

Wannan kuwa yabiyo bayan sanarwar da Bankin duniya ya bayar kwanan nan ne, inda yace agaji na tafiya ne tare da kyawanan manufofin tattalin arziki. Akasarin Kasashen dake bada agajin kuwa suna samun ka 'idojun aikin su ne daga shi Bankin duniya.

Binciken da jami'ar Nottingham ta gudanar kwanan nan, karkashin jagorancin sashin kula da aiyukan raya kasa na duniya dake Biritaniya ya goyi bayan shawarar ta Bankin duniya. Binciken ya nuna cewa rashin daidaito ga agajin da kasashe ke samu yafi ga cigaban tattalin arzikin su.

Taimakon kudi a koda yaushe anayi ne da nufin zuba jari, amma masu zuba jari suna fargaba in har agajin bai zuwa a kan kari, inji Oliver Morrissey, wanda yana daya daga cikin wadanda suka bada rahoton. Yawan rashin cigaban tattalin arziki. Binciken yayi kuma nazarin dagantakar dake tsakanin rashin tabbas wajen bada agaji da cigaban tattalin arziki tare da misalai daga kasashen 88 masu tasowa.

Kamar yadda nazarin ya nuna rashin tabbas ga agaji zaishafi tattalin arziki a hanyoyi biyu. Na farko yana iya nuna kasa bata da daidaito kan cigaban tattalin arziki irin yunwa. Ko ambaliya ko rashin daidaito kan farashin kayan abinci. Na biyu rashin daidaito na iya dagula manufar zuba jari ga kasa.

Bugu da kari kuma binciken ya nuna rashin tabbas na rage kaifin samun agaji dakuma marowar tattalin arziki.

Daga cikin matakan da aka gabatar domin gyara sun hada da inganta manufar tattalin arziki a kasashen dake karbar agaji, da samun kasashe zaunanu dake bada agajin dakuma bada fifiko ga kasashen dake kokarin daidaita harkokin su na tattalin arziki.
*ID2/Obasi Ogbonnaya*

**Sare Itacen Katako Ba Bisa Doka Ba A Tanzania Na Barazana Ga Dajin Kasar** **2mins 19secs**

Tanzani na asarar kimanin kadada dubu dari biyar na gandun dazuzukan ta masu amfani kowace shkara saboda masu sare itacen katako. Wannen kuwa kamar yadda aka buga a wata jarida da akayiwa lakani 'Sare Ka Gudu' Sare katako ba bisa doka ba da sana a katako a yankuna mai zafi, jaridar tace jami'an Gwamnati suna daga cikin masu irin wannan laifi wanda ya sanya kasar mai kadadamiliyan 33 da dubu dari biyar cikin hatsarin gaske.

Sare gandun dazuzzuka ba bisa doka ba da cin hanci da jami'an gandun dazuzzuka keyi da na jami'an kostom suna daga cikin abubuwan dake fuskanta har ma da kasashe irin su Kenya da Senegal, da Ghana da Naijeriya dakuma Camerou.

Jaridar tace Tanzaniya bata da kuzarin tabbatar da kare gandun dazuzukan ta. Da yake maida martani bisa wannan rahotan Firayi Ministan Tanzaniya Fredrick Sumaye ya sha alwashin sanya kafar wando guda da dillalan katako ba bisa ka'ida ba.

Babban sakataren ma'aikatar albarketun kasa da yawon bude ido Philemon Luhanjo yayi na'am da cewar wasu jam'an gandun daji suna da laifi kan cinikin katako ba bisa doka . Haka kuma ana zargin su da hada baki wajen cutar da dabbobin dake gandun daji sai dai yaki yarda cewar jami'an dake aiki a shain kula da dabobin dawa suna taimakawa masu cinikin fatun dabbobin ta hanyar kungiyar mafarautar Tanzaniya. Sauran wadanda ake zargi bisa wannan sana'ar dillalan katako da masu sarrafa katakon da sauran mutanen dake aiki a kamfanonin sarrafa itatuwan katako.

Luhanjo yace haka ma ana digba cuta a kusan dukkan kassar a dazuzukan da aka kebe da wadanda bia kebe ba. Wadanda ake zargin suna gudanar da aikin sune domin samar da katako ko itacen wuta ko gawayi.

A kokarin ta na hana irin wannan ta'asa, hukuma ta fara neman taimakon mazauna karkara dake kusa da gandun dazuzuka. Kuma saboda rashin zabi domin samun makamashi irin wadan nan mazauna karkara suke sare itatuwa domin yin girki. Yanzu ana ilmantar dau kan yadda zasu taimaka wajen kare gandun dazuzuka maimakon lalatawa domin amfani na dan takadirin lokaci.

Haka kuma 'yan sanda na sintiri akan manyan hanyoyi danufin tsare wadanda ake tuhuma dakuma kwace abinda suka dauka.
Enviromental News Network

**Ciyawa Mai Guba Na Barazana Ga Ciyayin Gabashin Afrika 2mins 12 secs**
Yankin kasar gabashin Afrika dake da dausayi da ciyayi masu kyau, dake kula da dabbobin dawa yanzu yana fuskantar barazana daga wata irin ciyawa mai guba.

Ita wannan ciyar da ake kira Tarcharantus dake yaduwa a kasa tana daidai da irin kainuwar nan dake addabar kogunada koramai a yankin Africa ta yamma yau kusan shekaru kenan.

Ciyawar tana saurin yaduwa a wannan yankin kasa kamar yadda rahoton da aka bayar kwanan nan a jaridar kasar Kenya, ciki kuwa harda yankunan dake da duwatsu da kwazazafai inda take girma tare da jijiyoyi masu karfi, wanda ke tauye albarakatun kasa, kana sauran ciyayin basa iya jure mata musamman ciyayi da akeyin magunmaguna dasu.

Ciyawar Tachanantus camphoratus wanda kabillar Msai ke kira ‘leleshwa’ an fara ganin ta ne kimanin shekaru 30 da suka wuce. Masana harkokin karkashin kasa sunce ciyawartana da wata irin baiwa na sabo da duk yanayin da ta sami kanta ciki, kana kuma bata da amfani. Tana kashe sauran ciyayi kuma ba a amfani da ita dabobi ma basa cin ta.

Masanan sunce ciyawar ta karu har sau hudu tun daga lokacin da aka fara ganin ta shekaru 30 din da suka wuce, india ta mamaye fili mai fadin kadada dubu dari da talatin a Kenya, kadai akasari a yankunano dake da kwazazzafai. A Laikipia dake yankin arewa ta tsakiyar Kenya yaduwar ciyawar ta tilastawa dabbobin dajin zuwa bakin sashin da ake kare su wanda hakan ya sanya ake samun matsala tsakanin dabbobin da masu dabobin gida asboda neman abincin da zasu ci. A yankunan da ciyawar ta leleshwa tayi kakagida kuwa dabobin dake yankin duk sun bace baki daya.

Wasu masana karkashin kasar sunyi gargadin cewar, in har ba ashawo kan leleshwa ba wsu sassan yankin savahna na gabashin Afrika Zasu Zama sahara. Amma kuma akwai alamun dake nuna cewa ciyawar tana da maiko a jikint, masana kimiya na bincike kan yadda za a sarrafa ta domin kasuwanci. Wannan shi ya sanya ake saran ciyawar za a shawo kanta domin noman ta a nan gaba.
*AWF Wildlife News*

# Rahonti

**Ghana Na Fuskantar Raguwar Kifi Cikin Hanzari 4 mins**
Masana’an tun kamun kifi na kasar Ghana suna fuskantar mawuyacin hali saboda yadda mazauna bakin ruwan kasar ke kamun kifi baji-ba-gani a sakamakon fasahar zamani na kamun kifi a teku. Alamar farko na wannan matsalar ta fara kunno kai ne a irin bukukuwan kamun kifi da aka saba yi a yankunan dake bakin ruwa inda ake shirya kayan abincin da akayi dashuwa da kifi iri-iri.

Baya ga iska mai sanyi babu kuma wata hujjar dake nuna cewar bukin kamun kifi yazo ya wuce kamar yadda wani dan rahoton kasar Ghana ya bayar. Yace dukkan bukukuwan kamun kifin kasar sun zi har sun wuce babu kifin dake tukunya koda karfasa ne. Ba da jimawan nan ba ne bukin kamun kifi na herring mastina ke sake maida kifin da suka kama cikin teku saboda rashin kasuwa.

Domin baiyana tsananin karancin kifin har yanzu an shiga tsatubar al'ada. Masinta dake kauyukan dake kusa da brinin Accra sun dora laifin rashin samun isashen kifin ne kar shirin kayyade iyali tsakanin kifayen. Kauyawan dama can basa son maganar kayyade iyali suna daukar wannan batu danufin sake komawa bisa al'adar su ta tuntuni.

Yanzu haka kowani daya daga cikin aiki biyar na dan Ghana na fuskantar barazana akasarin su'sun shiga aikin kamun kifi ko kuwa said inji mukadashin darektan ma'aikatar kula da kifi ta Ghana Mr. George Hutchful, wanda yace babu annuri nan gaba.

Yawan kifin da ake samu sai kara raguwa yakeyi ainun, wanda hakan ya sanya ake kama kifin da basu kosa ba. Wannan kuwa ya haifar da koma baya ga irin kifin da ake samu, wanda ya sanya kudin da ake samu daga kifin ya ragu. Ya kuma dora laifin kan yadda masintaa Ghana basa bin ka'idojin da aka shimfida wanda suke samar da kusan duk kifin da Ghana ke bukata.

Mr. Hutchful yace kokarin da Gwamnati keyi na bullo da manufar kayyade yawan kifin da za arika kamawa (TAC) yana samun cikas saboda gasar dake akwai dakuma ingantuwar hanyoyin kamun kifi irin na zamani. Yawan kifin da aka amince a rika kamawa kowace shekara a Ghana shine ton dubu metan da goma. Amma kumma ba abin wannan ka 'idar.

Shekaru goma da suka wuce yawan kifin da ake kamawa yana tsakanin ton dubu dari uku da hamsin zuwa ton dubu arbamiyya. Mr. Hutchful yace ana kuma shigo da wasu kifin tondubu dari bakwai daga waje a duk shekara dominbiyan bukatun jama'ar kasar.

Kifi dai shine babban abincin mutanen Ghana domin samun abinci mai gina jiki musamman a manyan birane. Wannan matsalar kuwa zata kara tabarbarewa ganin irin halin da ake ciki. Nan da shekaru 20 masu zuwa fiye da rabin mutane miliyan 18 da Ghana ke dasu zasu kasance a birane ne. Hakan inji Mr. Hutchful zai kara yawan bukatar kifi kenan.

Kungiyoyin masintan kasar sun fara daukar mataki. Yanzu sun fara sanya wakila kungiyoyi yin yin rantsuwar ba zasuyi amfani da guba ba wajen kamun kifi. Kamar yadda sarkin tarun al'umar Mumford yace suna gudanar da rantsuwar ne ta hanyar yin amfani da burkutu, kan wan duk ya karya rantsuwar to kuwa aljanun ruwa zasu halakashi. Akwai sama da jiragen kwale-kwale masu inji kimanin dubu tara wanda rabin su na da na'urar kamun kifi a kauyuka 189 dake farfajiyar ruwayen kasar Ghana mai tsawon kilomita 550

A nata bangare, Gwamnati yanzu tana duba irin ragar da ake amfani dasu wajen yin su. Ance kamfanonin Korea ne ke da akasarin jiragen dake kamun kifi a tekun ruwayen kasar ta Ghana. Wannan mataki kuwa kwalliya ta fara biyan kudin sabulu, domin daga cikin biyar ana kame hudu na tarun da ake dubawa a tashar jiragen ruwan Tema da ma'aikatar kula da kamun kifi ke aiwa tarwa.
*Edward Ameyibor*

**Ma'aikata A Kasar Mali Sunyi Nasarar Karin Albashi** **3 mins 30 secs**
Ma'aikata a kasar Mali sun sami karin kashi 7 cikin dari na albashin su bayan nasarar da suka samu na yajin aikin da sukayi karkashin babbar kungiyar kwadagon kasar (UNTM).

Yajin aikin ya cimma fiye da karin albashi da ya fara aiki daga watan Oktoba, haka kuma za a sake duba tsarin albashin ma'aikatan Gwamnati, wanda zai fara daga watan Janairu shekera mai zuwa. Wata tawagar kwararu kan tattalin arziki ne zai duba tsarin albashin tare da jami'an Gwamnati dana babbar kungiyar kwadagon kasar, wanda Ministan aiyukan Gwamnati Zai zabo su.

Bugu da kari yarjejeniyar da aka kulla da Gwamnati ta tabo wasu sassan kula da jindadin ma'aikatan ciki harda kula da farashin kayayyakin abinci, wanda yayi tashin gwauron zabbi da kashi 10 cikin dari a shekera, da kuma ragi kan kilowatt na wutar lantarki da ma'aikatan na Mali ke saya. Akasarin yarjejeniyar da aka kulla sun fara aiki ne batare da jinkiri ba.

Wannan sabon tsarin wanda ya fara aiki nan take yana kara karfafa gwiwa inji wani wakili a kungiyar kwadagon kasar.

Duk da haka wasu ma'aikatan suna nuna fargabar su kan farashin wasu muhimman kayan zai tashi nan gaba kadan saboda karin albashin. 'Zamu tsaya muga yadda 'yan kasuwa zasuyi da hajar su game da karin albashin, domin kuwa in har sun kara farashin kayan su, to kuwa za a koma gidan jiya ne inji wani wakilin babbar kungiyar kwadagon UNTM, wanda ya sha jinin jikin sa duk da yabon da jaridun kasar keyi na cewar wannan babban abin tarihi ne. Ya tuna a shekarar 1994 yadda akayi karin kashi 10 cikin dari na albashi saboda rage darajar takardar kudin CF, wanda ya sanya kwalliya bata biya kudin sabulu ba saboda karin farashin kayayyakin masarufi. Yazuwa yanzu dai farashin kayan na nan kamar yadda suke ada a kasuwani.

Mahmoudu Bathily, wanda ke shiga tsakani wajen tattaunawar karin albashin na UNTM ya bada tabbacin cewar farashin kayayyaki zai tsaya kamar yadda yake yanzu, kana za a shawarci Gwamnati in bukatar hakan ta taso domin dakile tashin farashin kayan.

Karin albashin na nufin baiwa ma'aikata damar cin moriyar shirinne, wadanda yanzu haka suke karkashin matsin lambar. Bazata sabu ba in har farashin kayan masarufi kamar su masara da hatsi, da man girki da man gas suka tashi wanda zai shafi irin na nasararda muka samu inji Bathily.

A nashi bangare Sidibe yayi alkawarin ganin cigaba da rike yarjejeniyar da aka kulla da shugabanin kungiyar kwadagon.

Sauran kungiyoyin ma'aikata ma sunyi maraba da karin albashin, irin su kungiyar hadin kasa na ma'aikatan Mali (CSTM)wadda taki shiga yajin aikin. Shugaban CSTM din Amadou Amion Guidon yace koda shike karin albashin matakin farko ne amma bai wadatar ba ma'aikata zsau cigabada fafutuka.

Kungiyar ta CSTMtana shirin gudanar da nata yajin aikin domin bukatar kawo karshe karancin wutar lantarki, wand ke jefa kasar cikin mawuyacin hali. Haka sumama'aikatan dake aiki a kamfanoni masu zaman kansu na shirin gudanar da yajin aiki, domin neman karin albashi, wanda suka kasa samu ta hanyar tattaunawa..

**Madagasca Ta Kaddamar Daa Sabon Gandun Daji Na Kasa 3mins 11 secs**

Yanzu haka gandun dajin Andringitra dake Madagasca ya kammala domin masu yawon bude ido. An kaddamar da gandun dajin ne cikin watan Oktoba, kuma anyi alkawarin zai sami nasara kamar yadda hukumar WWF take kokarin ganin an kirkiro da gandun dajin tare da wasu kungiyoyi. Kungiyoyin kuwa sune kungiyar kula da yankunan da aka kebe na kasa (ANGAP), da Gwamnatin Madagasca dakuma kungiyar bada agaji ta kasar Jamus, KFW.

Shidai gandun dajin Andringitra na da fadin kadada dubu 31 da 160 yana kwance ne tsakanin wasu tsoffin yankuna biyu da aka kebe watau yankunan Ranomafana da Isalo. Daga cikin abubuwan sha'awar dake ciki sun hada da manyan tsaunuka da dabbobi dakuma yanayi iri uku, kamar su yankin daji mai yanayin zafi, da yankin daji mai dausayi da kuma yankunandake da duwatsu da tsaunuka. Kana wani abin baba sha'awar kuma shine kolouwar dutse mai tsawon mita dubu 2 da dari 6 da 58 shine kuma dutse na biyu mafi girma a kasar baki daya kuma yana da mashigi.

Wannan sabon yankin da aka kebe nada wuri mafi kyau da wannankasa na tsibiri ke iya bugun kirji dashi. Huumar WWF ta fadi cikin sanarwar da ta bayar ranar 8 ga Oktoba' Yankin mafi kyau da albarkatu zai kuma bada dama gudanar da bincike da yanayi tare da ilmantarwa da ynakunan dake da duwatsu.' An tanadi wurare masu tsawo kilomita 40 dakuma wasu sansanoni daban-daban guda hudu cikin gandun dajin.

Aiyukan da akayi ta gudanarwa a gandun dajin na Andringitra tun 1993 anyi ne da nufin karfafa gwiwar masu sha'awar au\iyukankula da muhalli da halittu a yankunan da aka kebe su. Mazauna yankunan karkara suna shiga cikin shawarwarin yadda za a tafiya da gandun dajin ta yadda za arika kulawa dakuma kare yankin.

Shirin kula da dajin na kasa shine na raya yankin domin yawon bude ido, wanda zai kare albarkatun dake akwai a yankin dakuma taimakawa kan harkokin tattalin arziki da zaman takewar mazauna yankin, tare da inganta bukatun al'adun su.

'Baya ga 'yan kalilan na yankin dake sashin kudu da kudu maso yamma na tsibirin Andringitra yana matsayin samfur na irin albarkatun kasa: ofishin hukumar WWF a kasar Madagascar Mr. Lantosoa Ramarojaona.

Fiye da mutane dubu 15 a kauyuka 196 ke zaune yankin da gandun dajin yake kuma sun shiga cikin aikin gadan-gadan.

Wata kila babban karfi da aikin ya samu shine goyon bayan da kabilun Betsileo da Bara dakuma Tanala suke baiwa shirin inji darektan aiyukan Joseph Ralaiarivony. Yace sun baiwa shirin goyon baya t hanyar kyalewa a gudanar da aikin a yankunan su bisa al'adun su ta yadda suke kare gandun dajin. Saboda irin kudurin da suke dashi ya sanya aikin ya kasaita.
*WWF*

# Sashin Yara

**Zamanin Da Bauna Ke Farauta** **5mins 10secs**

(Cikin littafin tatsuniya na kabilar Bushman dake kudancin Afrika, da can Bauna tana cin nama ne kuma sauran dabobi na tsoron ta).

A wani zamani anyi wata Bauna katuwa mai ban tsoro dake zaune kusa da wani kududufi. Baunar tana farautar namum daji domin samun abin kalace, tana kuma da wasu kaho da sauran namun dawa ke tsoro. Saboda wannan karfin nata ba wadanda suke cika mata ido baya ga Giwa da karkanda.

Wata rana Batunar ta sami zaki na shan ruwa batare da sani ba, Baunar na kokarin kashe zakin da kahon ta, sai zaki ya durkusa ya roke ta kan ta ji tausayin sa kada ta kashe shi, Bauna ta yarda Zata kyale shi amma bisa sharadin cewar, zakin zai zama bawan ta kuma shi zai rika zuwa yana farauto mata naman da zata rika ci. Zaki ya amine tunda baida wani zabi.

Domin haka Bauna ta cigaba da baiwa zaki umurnin zuwa yi mata farautar naman dawa wadanda ke kiwe, a wannan dajin yana kawo mata tana ci ko yaushe. Domin haka Bauna tace wannan tsari yayi mata daidai, domin sai tayi kwanciyar ta kawai tana hutawa, shi kuwa zaki yana yi mata farautar namun dawa yakawo mata tana kwance abin ta.

Ranan sai Bauna ta kira zaki ta umurce shi da yaje ya kawo mata dan alfadari domin shi take kwadayin karya kumallo dashi, nan da nan zaki yaje ya kaso ya kawo Bauna ta cinye dan alfadarin nan kaf batabarwa zaki koda dan kashi ba ya taba.

Bayan nan kullum sai Bauna ta umurci zaki da ya kaso mata namun daji dayawa domin hadama, komai bata baiwa zaki saboda hidimar da yakeyi mata. A halin yanzu saboda zaki ya maida hankali wajen hidimar Bauna sai matan sa da 'ya' yan sa duk suka fara galabaita musamman yaran zakin yunwa ta fara cin su. Yayinda iyalan zaki suke kara ramewa, ita kuwa Bauna sai kara kiba da karfi takeyi. Har takai ga Bauna ta fara cin abinci sau biyar kowace rana, inda zaki ke sama mata.

Wata rana Bauna ta sami zaki na kwance karkashin inuwar bishiya. Ta umurce shi da ya tashi ya shirya zuwa farauta, tunda Bauna tayi kiba ainun dakyar take tafiya. Haka kuma kahunan ta sun girma sosai.

Yau inji Bauna tace da zaki ina so ka shiga daji ka kaso kowani nau'in dabba daya dake cikin dajin nan. Nan da nan zaki ya ga wannan ba karamin aiki bane musamman da ya yanzu duk ya galabai ta ga rashin hutu. Sai yace ranki dade ai wannan abu ne dake da matukar wuya kin san ba zai yiwu ba. Zaki yace gashi kuma iyali na duk sun galabaita, yunwa ta kassara su banda wani lokacin kaina domin kulawa dasu saboda aikin ki. Domin haka ranki dade nake rokon ki da ki taimakeni kyale ni haka domin inje in kula da iyali na.

Amma saboda hadama irin na Bauna sai ta fusata taki tausayawa zaki. Tace na ki kashe ka ne kwanakin baya saboda alwawarin da ka dauka ta fada a fusace. Domin haka tilas ne ka aikata abinda na umurce ka da kayi. Nan da nan Bauna ta sanya kahon ta ta karci kasa ta tada kura sama.

Sai zaki ya tashi tsaye. Ya san cewa babu sauran mafita cikin wannan sh'ani sai ya yanke shawara a zuciyar sa. Yace ya ke Bauna tila ne na aikata abinda kika umurce ni domin alkawari ne na dauka. Saboda hadamar ki zan kashe daya daga cikin dukkan nau'in dabobi dake cikin wannan dajin. Kuma zan fara ne dake saboda kina daya daga cikin na'in dabbobin.

Domin haka sai zaki yayi kukan kura ya aukawa Bauna a bayan ta ya kafa hakoran sa jikin ta da wuyar ta kafin kace meyen haka Bauna ta mutu.

Daga karshe zaki da iyalen sa suka sami kansu cikin naman Bauna faca-faca sukayi ta ci. Kuma tun daga wannan lokaci ne zaki ya fara farautar Bauna. Kuma darasin da Bauna ta koya daga nan sai ta fara cin ciyawa ta daina cin naman dabbobi. Kuma Bauna ta yanke shawara kasancewa a garke-garke maimakon yawo dai-dai, domin kare kansu daga sarkin dawa watauzaki
*When Hippo Was Hairy*

**Dalili Dakuma Yadda Jalbe Ke Huda Bishiya Busashiya 1min 2 secs**
Jalbe tsuntsaye ne dake da dogon baki mai kauri da karfi wanda ya hade da kashin kan su. Haka Allah yayiwa jalbe baiwa domin ya rika zama a wuraren dake da busasun bishiyoyi.

Yayinda akasarin tsuntsaye na zama ne a gidajen su da sukeyi da ciyayi da gashi jalbe na gidan sa ne hanyar yin rami a jikin busashiyar bishiya. Haka kuma suna yin kafofi a jikin bishiyoyin ta yadda zasu sami damar kama kwari da tsutsotsi domin abinci.

Ana samun nau'in jalbe daban-daban a Afrika ciki harda masu geme da masu filafilai. Jalbe mai geme an sanshi da yin wasu abubuwa kuma daban da wannan baki nasa. A duk lokaci da ya fara kada fila-filan nan nasa to fa yana aikawa da sako ne. Inda yake nuna cewa, n an ne gida na.

**Yaya Karkanda Ke Kare Kansa Daga Abokan Gaba 1min 11secs**
Karkandana da kananan ido kuma bata cika gani ainum ba don haka yaya take kare kanta? Duk da haka Allah yayi musu baiwar ji ainun dakuma sansana wanda yake taimaka musu wajen rashin gani sosai. Haka kuma karkanda na amfani da kahon ta wajen karen kan ta da 'ya'yan ta daga farmakin abokan gaba irin su zaki.

Da yake suna girma ainun karkanda basu cika samun abokan gaba ba. Duk da haka babu dabbar da zata kare kanta daga maharbi dake rike da bindiga ko mashi ko tarko. Saboda haka karkanda iri biyu da ake dasu a Afrika ake farautar su. Sune kuwa farar karkanda da bakar karkanda. Mafarauta sun fi farautar bakar cikin shekaru da dama inda suke saida kahon ga 'yan kasuwan kasashen ketare akasari kasashen Larabawa, inda ake amfani dashi domin maganin gargajiya dakuma wuka . Muddin ba munyi taka tsan-tsan ba tare da kula da 'yan bakaken karkandan da suka rage, zamu wayi gari mu rasa su baki daya.
*Chogololo*

**Rezar Mikiya** **2mins 7secs**

Can a wani zamani anyi wanti mikiya dake zaune a wani kauye tare da kawarta sa hankaka suna zaune. Wata rana sai hankaka taje wajen mikiya yua same ta ta fara gaishe ta bayan nan yace na zo ne na ari rezar ki domin zanyiwa yara na aski. Sai mikiya ta baiwa hankaka reza, kana hankaka ta koma gida ta askewa ya'yan ta gashi. Bayan da ta kare sai ta ajiye rezar a wurin da ya dace inda ba zaia bata ba domin maidawa da mikiya daga bisani. Amma sai karamin dan ta ya dauki rezar ya tafi da ita waje yana wasa, har ta bata.

Bayan 'yan kwanaki lokacin da mikiya ke bukatar amfani da reza domin yiwa 'ya'yan ta aski, sai ta je ta tambayi hankaka rezar ta. Sai hankaka ta shiga neman reza. Sai mikiya da hankaka basa kawance. Domin in mikiya na wuri sai kaga hankaka ta kidime tana neman inda zata sanya 'ya'yan ta, kuma sai kaga tana nema ko ina domin gano rezar mikiya.

*Shangani Folktales*

## Sashi Na Musamman

**Karin Maganar Muhalli** **15secs**

'Babu abinda yafi muhimmanci irin karantar da 'yan baya masu zuwa kyawawan halittu da yanayin dake akwai tsakanin al'umomin duniya , duniyar dake fuskantar barazanar jahilcin mutane da bambanci'

*Sir Peter Scott (Masani Kan Yanayi)*

**Kungiyoyin Masu Zaman kansu Na Kokarin Zama Da Gindin Su A Sri Lanka** **2mins 17 secs**

Kungiyoyi masu zaman kansu a Sri Lanka sun ja damara domin takawa Gwamnati burki kan yadda take tauye musu 'yancin hulda da kungiyoyi. Kwanan nan ne Gwamnatin kasar ta kafa kwamitin kulawa da aiyukan kungiyar bada agaji ta Red Cross ta kasar (SLRC). Wannankuwa shine karo na biyu da ma'aikatar kula da walwalar jama'a ta kasar ta kafa irin wannan kwamiti cikin watan Maris a sakamakon zargin sama da fadi da rashin iya tafiyar da aiki cikin kungiyar da akayi.

Sabon kwamitin an nada shine bayan da Gwamnati tayi gyara cikin watan Mayu ga dokar aiyukan sa kai na kungiyoyi masu zaman kansu na shekarar 1980, wanda akafi sani da dokar kula da kugiyoyi masu zaman kansu. (NGO)

Kungiyoyi masu zaman kansu sama da 500 ne suka sanya hannu bisa takardar dake kira ga Gwamnati kan ta soke wannan dokar. Gyaran dokar da kafa kwamitin duk kungiyoyin sunyi tir dasu, wanda suka ce wani ci baya ne ga kokarin kungiyoyin.

Doka ta zama shishigi ne cikin harkokin kungiyoyin inji wasu 'yan kungiyaar, domin dokokin da a ake dasu tuntuni sun isa wajen gudanar da binciken almubazziranci cikin kungiyoyin tare da hukunta duk wanda aka samu da laifi.

Fidda mutanen dake rike da mukamai cikin kugiyoyi masu zaman kansu bisa zargin da akeyi musu tare da maye gurbin su da wasu mutanen da Ministan kula da ma'aikatar walwalar jama'a zaiyi kamar yadda akayi a kungiyar bada agaji ta Sri Lanka, zai iya sanya yin aiki da iko fiye da kima inji sanarwar da wata jarida mai zaman kanta a Sri Lankan MIRJE ta bayar.

A halin yanzu kuma ana zargin wakilan kwamitin da Gwamnatin ta nada na farko domin sa ido kan kungiyar bada agajin ta SLRC. Ana zargin su da laifin biyan kansu wasu makudan kudin alawus, amfani da motoci kungiyar domin amfanin kansu dana iyalan su haka kuma wasu daga cikin iyalan wakilan suna bulaguru zuwa kasashen waje domin karo ilmi, wanda iyalan'yan kungiyar na asali ya kamata suyi haka, SLRC.
*BAOBAB*

**Shekaru Biyar Bayan Taron Beijin** **1min 38secs**
Wakilan Gwamnatoci zasu hadu a wani taro na musamman na babban zauren majalisar dinkin duniya domin nazari cikin watan yunin shekara 2000 yadda aka aiwatar da kudurin da aka zartar a babban taron mata na duniya da akayi a Beijin kasar sin a shekarar 1995. Duk da haka kungiyoyi masu zaman kansu da suka shafi mata sun fara kira ga Gwamnatoci da su aika da wakilan su wajen taron da hujjoji dake nuna cewar sun soke dokokin dake nuna bambanci tsakanin maza da mata. Biyu daga cikin irin wadan nan kungiyoyin watau DAIDAITO YANZU dake Washington D.C kasar Amurka da YEKUWAR KAWO KARSHEN NUNA BAMBANCI GA MATA CEDAW.

Kirian yabiyo bayan kungiyoyin 'yantar da mata ke fadin cewar irin wadan nan dokokin suna nan daram da gindin su.

Yekuwar mu zatayi kira ga Gwamnatoci da su soke wannan dokar ko kuwa suyi gyara domin shekara mai zuwa, watau shekaru biyar bayan taron Beijin. A wajen wannan taro na musamman ne za a tabo irin wadan nan dokokin, danufin ganin an aiwatar dasu bawai kawai fada da fatar baki kawai ba, inji kungiyar DAIDAITO YANZU.

Wata mace mai fafutukar neman 'yancin mata Brooke Ackerly kuma farfesa a fanin kimiyar siyasa a jami'ar California ta kasar Amurka tayi imanin cewar hakkin mata yayi ya shige maganar dokokin daka nuna bambanci, ya maida hankali kan dalilai dakuma yadda abin ke shafar keta haddin matan.
www.equality.com

**Keta Hakkin Mata a Sassa Daban? Daban Na Duniya India** **1min 26secs**
Wata yarinya 'yar shekera 10 ta tsallake rijiya da baya, yayinda wata ma'aikaciya jirgin sama ta ceto ta yayinda ta ganta cikin jirgi tana kuka.

Ma'aikaciyar jirgin daga bisani ta gano cewar tana kuka ne saboda mahaifin ta ya saida ita ne ga wani tsohon balarabe dan kasar Saudi Arabia dan shekaru 60 dake zaune kusa da ita akan kudi dalar Amurka 240.

**KENYA**

- A wata makaranta da dalibai ke kwana, wasu dalibai maza su 300 suka shiga dakin kwanar dalibai mata da karfin tsiya, sukayiwa wasu 'yam mata saba 'in da daya fyade. Goma sha -9 aka tattake su suka mutu a kokarin da sukayi na tsirar da kansu.
  Mataimakin shugaban makarantar daga bisani yace yaran ba sunje ne da nufin jiwa 'yam matan lahani ba. Sunje ne kawaidomin yiwa 'yam matan fyade.

**BRAZIL**

? Wani mutum da ya furta da bakin sa cewar ya soki matar sa da wuka da wani farkar ta har lahira kotu ta sallame shi inda dukkan alkalan kotun maza ne. An sallame shi ne bisa hujjar cewar ya aikata laifin ne domin kare martabar sa da wani ke tauyewa.

**AMURKA**

? An soki wata mace 'yar shekaru 51 har goma sha-9 inda aka kashe ta. Kuma wani tsohon farkan ta ne, yayinda take zaune a cikin kotu tana jiran sakamakon shari'ar da akeyi mata. Wanda har sau biyu ana watsi da karar da ta shigar domin kare kanta.

*Equality Now*

**Hedkwatar Yiwa Mata Fyade Ta Duniya** **1min 31sec**

Yanzu haka dai an baiyana kasar Afrika ta kudu da cewar itace hedkwatar da akeyiwa mata fyade a duniya. Wannan kuwa ya biyo bayan kididdigar da aka bayar kwanan nan ne daga kasar, wanda ta nuna cewa fiye da kararraki dubu hamsin ne aka samu na yiwa mata fyade cikin shekara guda. Wata majiyar 'yan sanda tace adadin bai hada da wadanda suka faru bisa rashin sani ba. Sama da kashi 93 cikin dari na irin fyaden da ke faruwa ba a shaidawa 'yan sanda, kodai saboda tsoro ko kunya ga wadanda suka fada cikin irin wannan ta'asar.

Kamar yadda rahoton da aka bayar ta gidan rediyon Muryar Amurka (VOA) fyaden na hade da cin zarafi da tozartar da matan.

Cin zarafin da yafi daukar hankalin jama'a shine na wata mace da aka kama aka rufe mata ido da kyalle,wasu zaratan samari, suka kaita wani wurin sukayi ta lalata da ita har na tsawon kwanaki biyu, kana daga bisani suka yarda ita, inda wani mutum ya ganta. Hancin ta ya kone da leban bakin ta kuma tayi targade a wurare da dama na jikin ta tare da kujewa a duk jikin ta.
Ma'aikatan kiwon lafiya sun ce tana cikin wani irin mawuyacin hali na jin jiki zata kuma bukaci yin aiki a jikin ta.

Mataimakin shugaban kasar Afrika ta kudu Dr. Jacob Zuma, ance shine mutumin da yafi nuna damuwar sa kan aikata irin wannan laifin.

Amma masu zargin Gwamnati sunce dalilin da ya sa shi Dr. Zuma Ke nuna damuwa kan laifin yiwa mata fyaden saboda shima kwanakin baya wasu katti sun auka gidan sa dake can garin su a lardin Kwa-Zulu Natal, inda sukayiwa matar sa fyade.

# Kalmomin Da Akayi Amfani Da Su

| | | |
|---|---|---|
| **ANGAP** | - | Kungiyar Kular Da Yankunan Da Aka Kebe Ta Kasa |
| **CEDAW** | - | Yekuwar Kawo Karshen Nuna Bambanci Tsakanin Maza Da Mata |
| **CFA** | - | Kungiyar Kula Da Kudade Ta Afrika |
| **CSTM** | - | Hadiyar Kungiyar Ma'Aikatan Kasar Mali |
| **D.C** | - | Gundumar Colombia |
| **DFID** | - | Ma Aikatar Raya Kasa Ta Duniya |
| **DSA** | - | Kungiyar Nazarin Cigaban Kasa |
| **GNP** | - | Karuwar Kayan Masana'Antu Na Kasa |
| **KTW** | - | Kungiyar Bada Agaji Ta Kasar Jamus |
| **NCRC** | - | Cibiyar Bincike Kan Halittu |
| **NGO** | - | Kungiyoyi Masu Zaman Kan Su |
| **ODA** | - | Aiyukan Agajin Raya Kasa |
| **OECD** | - | Kungiyar Hadin Kan Tattalin Arziki Da Raya Kasa |
| **TAC** | - | Adadin Da Aka Yarda Kamawa |
| **UNTM** | - | Kungiyar Kwadago Ta Kasar Mali |
| **U.K** | - | Hadadiyar Daular Biritaniya |
| **U.S.D** | - | Dalar Kasa Amurka |
| **UWEP** | - | Shirin Kauda Shara Na Alkari'a |
| **WWF** | - | Asusun Kare Halittu Na Duniya |